Jerin Littafan Shi'a Na 4

# Auren Mutu'a

## a wajen

# 'Yan Shi'a

Umar Labɗo

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَنِ الرَّحِيمِ

## Ma'anar Mutu'a: Auren Wucin Gadi

Mutu'a, ko kuma auren wucin gadi, watau auren da ba na dun-dun-dun ba, ma'anarsa shi ne namiji ya ƙulla jinga da mace cewa zai sadu da ita sau ɗaya ko sau biyu, ko kuma na tsawon awa ɗaya, ko kwana kaza, ko wata kaza, a kan kuɗi kaza ko ladan abu kaza.

Auren Mutu'a yana cikin aurace-auracen Jahiliya kuma an yi aiki da shi a farkon Musulunci kana daga bisani aka haramta shi. An karɓo ruwaya daga Ali binu Abi Ɗalib (R.A), cewa "Manzon Allah (SAW) ya hana auren Mutu'a da cin naman jakin gida a lokacin (yaƙin) Khaibar."[1]

Amma 'yan Shi'a sun ci gaba da halasta Mutu'a kuma sun ƙago ruwayoyin ƙarya waɗanda suka nuna falalarta da ɗumbin ladan wanda ya yi ta, da kuma darajarsa a aljanna. Babu shakka sun yi haka domin su ɓata al'ummar Musulmi ta hanyar yaɗa lalata da ɓarna da alfasha a tsakaninsu kuma don su jawo hankalin jahilai, musamman matasa, zuwa ga tafarkinsu.

## Falalar Mutu'a

Akwai ɗaruruwan ruwayoyi a cikin littafan malaman Shi'a da suke izna da su waɗanda suke nuna falalar auren wucin gadi. Ya zo a cikin littafin **Man La Yahduruhul Faƙih**, ɗaya daga cikin littafansu guda huɗu mafiya inganci, sun laƙa ma Ja'afar Sadiƙ, Imaminsu na shida, cewa ya ce: "Lallai Mutu'a addinina ce kuma addinin iyayena. Wanda ya yi aiki da ita

[1] **Bukhari** da **Muslim.**

ya yi aiki da addininmu kuma wanda ya yi inkarin ta ya yi inkarin addininmu, kuma ya yi riƙo da wanin addininmu."[1]

Ya zo a wannan littafi har yau, sun dangana ga Annabi (SAW) cewa wai ya ce: "Wanda ya yi Mutu'a sau ɗaya zai amince fushin Allah, wanda ya yi Mutu'a sau biyu za'a tashe shi tare da zaɓaɓɓun bayi, wanda ya yi Mutu'a sau uku zai haɗa kafaɗa da ni a aljanna."[2] A wata ruwayar mai kama da wannan, sun ƙaga wa Manzon Allah (SAW) cewa wai ya ce: "Wanda ya yi Mutu'a sau ɗaya za ta zama (gare shi) kamar darajar Hussaini (A.S); wanda ya yi Mutu'a sau biyu darajarsa kamar darajar Hassan (A.S) ce; wanda ya yi Mutu'a sau uku darajarsa za ta kasance kamar darajar Ali (A.S); kuma wanda ya yi Mutu'a sau huɗu darajarsa kamar darajata ce."[3]

Da yake mata suna da ƙarin kunya a kan maza, wataƙila za su buƙaci a ƙara ɗan ingiza su kaɗan kafin su faɗa ramin alfasha. Don haka Alƙummi, wanda suke yi wa laƙabi da Alsaduƙ (watau mai yawan gaskiya!) ya kitsa musu tasu ruwaya ta musamman. Ya ce, "Lokacin da aka yi isra'i da Annabi (SAW) zuwa sama, ya ce: Jibrilu ya riske ni ya ce: Ya Muhammad, Allah mai girma da ɗaukaka yana cewa: Lallai ni na gafartawa masu yin Mutu'a daga matayen al'ummarka."[4]

## Ladan Mai Yin Mutu'a

Abinda ya gabata dangane da falala da ɗaukakar darajar mai yin auren Mutu'a ne. Amma dangane da ɗumbin ladan da zai samu, bari mu saurari Alsaduƙ ya ƙara shara mana ita. Ya ce: an tambayi Abu Abdullahi, watau

[1] Ibnu Babawaih Alkummi, **Man La Yahduruhul Fakih**, bugun Darut Ta'aruf, Bairut, 1401 B.H., mujalladi na 3 shafi na 336.
[2] A duba **Man La Yahduruhul Fakih** na Alkummi, muj. na 3 sha. 336.
[3] Fatahallah Kashani, **Tafsiru Minhajis Sadikin**, bugun Maktabatus Sadar, Tehran-Iran, 1379 B.H., muj. na 2 sha. na 493.
[4] A duba **Man La Yahduruhul Fakih**, muj. na 3 sha. na 463.

Imamin Shi'a na shida: Shin mai yin Mutu'a yana da lada? Sai ya ce, "In yana nufin yardar Allah da ita (Mutu'ar) ba zai yi magana da ita ba (matar) kalma guda face Allah ya rubuta masa lada da ita (kalmar), kuma idan ya kusance ta sai Allah ya gafartar masa zunubi, kuma idan ya yi wanka Allah zai gafarta masa da gwargwadon ruwan da ya shuɗe a kan gashinsa."[1]

## Gargaɗi ga Wanda Ya Ki Yin Mutu'a

Bayan bayanin falala da garaɓasar Mutu'a, idan da akwai wani mai taurin kai wanda ya ƙi ɗibar wannan garaɓasa, to sai a yi masa gargaɗi kuma a tsoratar da shi. Wannan shi ne abinda malamin Shi'a, mai suna Alfailul Kashani, ya yi a yayin da ya ruwaito daga Annabi (SAW) cewa wai ya ce: "Wanda ya fita daga duniya bai yi Mutu'a ba, zai zo ranar Alƙiyama yana yankakke (watau naƙisin halitta)."[2] A harshen Shari'a, irin wannan gargaɗi ana yin sa ne ga wanda ya aikata kaba'ira, watau babban zunubi, kamar shaidar zur, ko gudu daga fagen fama, ko saɓa wa iyaye da sauransu. Saboda haka za mu fahimta a nan cewa, ƙin yin Mutu'a dai-dai yake da aikata kaba'ira. Kuma wannan babu mamaki idan muka dubi waccan ruwaya da ta gabata wacce take cewa, "Wanda ya yi inkarinta ya yi inkarin addininmu."

Wannan ya sa Sayyid Hussain Almusawi, wanda a da ɗan Shi'a ne kuma Allah ya shirye shi ya tuba, yake cewa manyan malaman Shi'a na wannan zamani, kamar su Sayyid Assadar da Alburujardi da Asshirazi da Alƙazwini da Alɗibaɗiba'i da Abu Harith Alyasiri da kuma uban tafiya,

[1] **Man La Yahduruhul Fakih**, muj. na 3 sha. na 336.
[2] A duba **Minhajus Sadikin** na Kashani, muj. na 2 sha. na 489.

Imam Khumaini, duka suna yin Mutu'a, kuma suna yin ta da yawa ba kaɗan ba![1]

A bisa mafi rinjayen zato, Rafilawan Nijeriya ma suna yin mutu'a, kuma Mutu'a na cikin hanyoyin yaudara da suke jawo hankalin jahilai da su, musamman matasa maza da mata, zuwa ga wannan tafarki nasu mai nufin rushe durakun al'umma.

**Ɗaurin Auren Mutu'a**

Domin mai karatu ya gamsu da cewa Mutu'a ƙofar zina ce kawai aka buɗewa mutane, bari mu duba yadda ake yin ɗaurin aure a tsarin Mutu'a. Auren Mutu'a ba ya buƙatar a samu wakilin "ango" ko waliyin "amarya", ba ya buƙatar shaidu; ba'a ma buƙatar kowa ya sani, kuma bai buƙatar wani ɓata lokaci. Da zarar an haɗu sai kawai a yi a gama!

Malaman Shi'a sun ruwaito cewa wani almajirin Imam Ja'afar Sadiƙ ya tambaye shi: "Ya zan ce da ita idan na kaɗaita da ita? Sai ya ce: Ka ce: Ina auren ki auren Mutu'a a bisa Littafin Allah da Sunnar Annabinsa; ba kya gado, ba'a gadon ki; kwana kaza kaza, ko shekara kaza kaza, a kan dirhami kaza kaza, sai ka ambata mata ladan da kuka yi yarjejeniya a kai, kaɗan ne ko da yawa."[2]

Ina son mai karatu ya lura da yadda mai tambayar ya yi tambayarsa: "Ya zan ce da ita idan na kaɗaita da ita?" A ina a duniya aka san aure a cikin kaɗaitaka, a keɓe? Babu wani addini a duniya, ko wata al'ada, inda ake aure a keɓe. Babu inda ake aure a sirri sai a addinin Shi'a.

---

[1] Sayyid Hussain Musawi, **Kashful Asrari wa Tabri'atil A'immatil Adhari**, bugun Darul Iman, Alkahira, 2002, sha. na 34-35.
[2] Muhammad binu Ya'akub Alkulaini, **Furu'ul Kafi**, bugun Darul Murtali, Bairut, 1428 B.H., muj. na 5 sha. na 455.

Wannan kawai ya isa ya tabbatar wa da mai karatu nisan wannan launi na aure da addinin Musulunci. A Musulunci, ana so a ɗaiɗaita labarin aure, a kururuta shi, a yaɗa shi, a kwaza shi, a yi talla da shi har duniya ta sani. Hadisai masu yawa sun zo da haka. Albani ma kaɗai, a cikin littafinsa **Adabuz Zifafi**, hadisai shida ya kawo, duka suna nuna wannan ma'ana. Ga biyu daga cikinsu don misali:

1. "Ku yi shela da aure."[1]
2. "Bambancin tsakanin halal da haram (a aure) buga ganga."[2]

Dubi yadda Manzo(SAW) ya kwaɗaitar a buga ganga, duk da ƙyamar da Musulunci yake ga kiɗa, don a kwarmata aure!

**Sadaki ko Lada?**

Abin sha'awa ne yadda malaman Shi'a ba sa kiran sadakin auren Mutu'a da sunan sadaki, sai dai su ce ***ujura,*** watau lada. Duk littafan da na duba ba inda suka kira shi da sunan sadaki. Wataƙila a cikin wannan akwai matashiya, amma fa ga masu hankali!

Bari mu kira shi yadda suka kira abinsu: Mene ne ladan auren Mutu'a? Suka ce an tambayi Abu Ja'afar, Imamin Shi'a na biyar, ya ce, "Dirhami zuwa sama."[3] Ɗansa kuwa, Ja'afar Sadiƙ, ya ce, "Tafi ɗaya na gari ko tafi ɗaya na dabino."[4]

Watau da Hausa muna iya cewa sadakin auren Mutu'a shi ne ƙwandala ko gwan-gwan ɗaya na garin kwaki! Akwai wani addini a duniya

[1] Albani ya ce **Ibnu Hibban** da **Dabarani** da **Diya'u Almaqdisi** duka sun ruwaito shi, kuma isnadinsa mai kyau ne. Duba **Adabuz Zifafi** na Albani, bugun Almaktabul Islami, 1409/1989 sha. na 111-112.
[2] Albani ya ce **Nasa'i** da **Tirmizi** da **Ibnu Majah** sun ruwaito shi da isnadi kyakkyawa. Duba **Adabuz Zifafi**, sha. na 111.
[3] A duba **Furu'ul Kafi** na Kulaini, muj. na 5 sha. na 457.
[4] **Furu'ul Kafi**, muj. na 5 sha. na 457.

da ya wulaƙanta mata kamar addinin Shi'a? Allah ya tsare matan Musulmi da irin wannan ƙasƙanci!

## Da Wa Ake Mutu'a?

Shin sai da Musulma kawai ake Mutu'a? A'a sam! A cikin daren 'yan Shi'a, ko kyankyaso ma nama ne! Don haka suka rawaito daga Imaminsu na shida, Ja'afar Sadiƙ, (Allah ya isar masa ƙarerayin da aka laƙa masa), wai ya ce, "Babu laifi mutum ya yi Mutu'a da Bamajusiya."[1] Kuma ana yi da Banasariya (Kirista) da Bayahudiya, kamar yadda suka ruwaito daga Imaminsu na takwas, Abul Hassan Ali binu Musa Rida,[2] Haka nan ana yi da karuwa domin, kamar yadda suka ce, sai ya hana ta karuwanci![3]

## Ana Yi da Matar Aure!

Dangane da yin Mutu'a da matar aure (watau matar wani) akwai ruwayoyi guda biyu masu ban mamaki waɗanda ya kamata mai karatu ya gan su da idanunsa. Ta farko an karɓo ta daga Falalu Maulan Muhammad binu Rashid, ya ce da Ja'afar Sadiƙ: "Ni na auri wata mace auren Mutu'a sai ya ɗarsu a raina cewa tana da miji. Da na bincika sai na samu ashe tana da miji. Sai Ja'afar ya ce: Don me ka bincika?!"[4] A wata ruwayar, sai ya ce, "Wannan (binciken) ba ya kanka. Abinda yake kanka kawai shi ne ka gaskata ta dangane da kanta." [5]

Ruwaya ta biyu ita ma Kulaini da kansa (watau Bukharin 'yan Shi'a) shi ne ya ruwaito ta. An karɓo daga Abanu binu Taglub ya ce: "Na ce da

---

[1] Abu Ja'afar Muhammad binul Hassan Aldusi, **Tahzibul Ahkam**, bugun Darul Adwa, Bairut, 1406 B.H., muj. na 7 sha. na 256.
[2] **Tahzibul Ahkam**, muj. 3 shafi na 144.
[3] **Tahzibul Ahkam**, muj. na 7 sha. na 253. Kuma a duba **Tahrirul Wasila** na Ayatullah Ruhullah Khumaini, bugun Darul Ilmi, Kum-Iran, ba tarihi, sha. na 295.
[4] **Tahzibul Ahkam** na Aldusi, muj. na 7 sha. na 253.
[5] **Furu'ul Kafi** na Kulaini, muj. na 5 sha. na 469.

Abu Abdullahi (watau Ja'afar Sadiƙ) ni ina tafiya a kan hanya sai in ga mace kyakkyawa kuma ba ni da tabbas ko tana da miji ko karuwa ce. Sai ya ce: Wannan (binciken) ba ya kanka. Abinda yake kanka kawai shi ne ka gaskata ta dangane da kanta."[1] (Watau idan ta ce ba ta da miji shi ke nan.)

Wannan yana nufin cewa shi ɗan Shi'a babu abinda ya dame shi! Idan al'amari ya motsa masa, to ko matar wa yana kamawa. Shin muna iya cewa waɗanda suke zaune tare da Rafilawa suna cikin hatsari? Amma ba wannan ne kawai hatsarin ba; ga wanda ya fi shi.

**Ana Yi da Karamar Yarinya!**

Ana yin Mutu'a da ƙaramar yarinya wacce ta kai shekara goma. An tambayi Abu Abdullahi, "Ko mutum na iya yin Mutu'a da yarinya ƙarama? Sai ya ce: E, sai dai idan ƙarama ce ainun ta yadda ana iya yaudararta. Aka ce: Nawa ne idan ta kai ba'a yaudarar ta? Ya ce: Shekara goma."[2]

Imam Khumaini, shugaban 'yan Shi'ar duniya na wannan zamani, ya yi wani ɗan ijitihadi a nan. Ya ce ƙaramar yarinya da jaririya duka ana iya yin Mutu'a da su amma ba da haƙiƙanin saduwa ba, sai dai da sumbata da runguma da kuma abinda ya kira 'cinyantaka' [*tafkhiz*], watau mutum ya sa zakarinsa a tsakanin cinyoyinta. Sai mai karatu ya gafarce mu saboda ruwaito wannan ɗanyar magana, maras daɗin ji, amma haka Imamin ya faɗi, kuma maganar tana cikin littafinsa da ya rubuta da hannunsa.[3]

Wannan ijtihadi na Imam Khumaini ba a ilmance kawai ya tsaya ba; a'a ya aiwatar da shi a aikace. Sayyid Hussaini Almusawi ya ba da labarin Mutu'a da Khumaini ya yi da wata yarinya mai shekara huɗu ko biyar a duniya, a lokacin da yake zaman gudun hijira a ƙasar Iraƙi kafin juyin juya

[1] **Furu'ul Kafi**, muj. na 5 sha. na 462.
[2] A duba **Furu'ul Kafi**, muj. na 5 sha. na 463; da **Tahzibul Ahkam** na Aldusi, muj. na 7 sha. na 255.
[3] A duba **Tahrirul Wasila** na Khumaini, muj. na 2 sha. na 241.

halin da ya shugabanta a Iran, a shekara ta 1979. Mai son ganin wannan labari filla –filla, sai ya duba **Kashful Asrari** na Almusawi, shafi na 35-37.

Ba wani abu ya sa muka bi diddigin wannan mas'ala ba sai don mai karatu ya san cewa mutanen da gaske suke. Allah ya yi mana ***Alam Nasharaha!***

## Mai Mutu'a, Matanka Nawa?

Amsa ta gaskiya, tsakani da Allah, ita ce: Ba iyaka! 'Yan Shi'a sun ruwaito daga Imaminsu na biyar, Abu Ja'afar, ya ce: "Mutu'a ba da mata huɗu ba ne kawai; domin ita (mace mai Mutu'a) ba'a sakin ta kuma ba ta gado, ba'a gadon ta. Ita mai jinga ce kawai."[1]

Har yau, sun ruwaito daga Imaminsu na shida, Abu Abdillahi, cewa an tambaye shi dangane da Mutu'a: Ana iyakance ta da mata hudu? Sai ya ce, "Ka auri dubu; su 'yan jinga ne kawai."[2]

## Luwaɗi Da Mata

Malaman Shi'a ƙazamai suna halasta yin luwaɗi da mata kuma suna dangana halaccin wannan ta'asa ga Imamansu a bisa ƙarya. Sun dangana haka ga Imaminsu na shida, Abu Abdillahi Ja'afar Sadiƙ. Suka ce wani almajirinsa mai suna Abul Ya'afur ya ce, "Na tambayi Abu Abdillahi(AS) dangane da halaccin mutum ya zakkewa mace ta duburarta. Sai ya ce: Babu laifi idan ta yarda."[3] Haka nan sun dangana halaccin wannan ƙazanta ga Imaminsu na takwas, Abul Hassan Musa Rida.[4]

---

[1] Abu Ja'afar Muhammad binul Hassan Aldusi, **Al'istibsar Fi Ma Ikhtalafa Minal Akhbar**, bugun Darul Kutubil Islamiyya, Tehran-Iran, 1390 B.H., muj. na 3 sha. na 147.

[2] A duba **Al'istibsar** na Aldusi, muj. na 3 shafi na 147; da **Tahzibul Ahkam** shi ma na Aldusi, muj. na 7 sha. na 259.

[3] A duba **Al'istibsar** na Aldusi, muj. na 3 sha. na 243.

[4] **Al'istibsar**, muj. na 3 sha. na 243.

Uban tafiya, Ayatullahi Ruhullahi Khumaini, yana daga cikin malaman Shi'a masu ganin halaccin al'amarin. Ga abinda ya ce: "Ra'ayi mafi ƙarfi, kuma mafi bayyana, shi ne halaccin saduwa da mace ta duburarta." Haka nan ya faɗi ba sayawa, ba sakayawa.[1]

Babu shakka wannan ra'ayi na 'yan Shi'a ya saɓawa Alƙur'ani mai girma inda Allah Maɗaukaki yake cewa, "To idan sun yi wanka (watau matayenku) sai ku je musu daga inda Allah ya umarce ku." (Suratul Baƙara: 222). Malaman Tafsiri sun haɗu a kan cewa abin nufi da ***'inda Allah ya umarce ku'*** shi ne farji, ba dubura ba. Haka nan kuma ya saɓa da hanin Annabi(SAW) inda yake cewa, "Kada ku zakkewa mataye ta duburarsu."[2]

Muna roƙon Allah Maɗaukaki ya tsarkake mazan al'ummar Annabi da matanta daga wannan ƙazanta ta Majusawa.

## Aron Farji

Manyan malaman Shi'a suna halasta aron farji. Sayyid Hussain Musawi ya yi bayanin ma'anar aron farji kamar haka: "Aron farji ma'anarsa shi ne mutum ya bayar da matarsa ko baiwarsa ga wani mutum dabam sai ya halasta gare shi ya ji daɗi da ita ko kuma ya yi duk abinda ya ga dama da ita. Idan mutum ya yi nufin tafiya sai ya bar matarsa a wajen maƙwafcinsa, ko abokinsa, ko kuma duk mutumin da ya zaɓa, sai ya halasta a gare shi ya yi abinda ya ga dama da ita a tsawon tafiyar mijinta."[3]

Don halasta wannan ɓarna, malaman Shi'a suna dangana ruwayoyi ga Imamansu a bisa ƙarya. Daga cikin irin waɗan nan ruwayoyi, akwai abinda suka dangana ga Abu Abdullahi. Alɗusi ya karɓo daga Abul Hassan Aɗɗari'i, ya ce: "Na tambayi Abu Abdillahi (A.S) dangane da aron farji, sai

[1] Duba littafinsa, **Tahrirul Wasila**, muj. na 2 sha. na 241.
[2] **Tirmizi** da **Nasa'i** da **Ibnu Maja** duka sun fitar da Hadisin.
[3] Sayyid Hussain Musawi, **Kashful Asrar**, sha. na 46-47.

ya ce: Babu laifi."[1] Har yau, Alɗusi ya karɓo daga Zuraratu, ya ce: "Na tambayi Abu Ja'afar (A.S) dangane da mutum ya halasta wa ɗan uwansa farjin baiwarsa. Sai ya ce: Babu laifi; abinda ya halasta masa daga gare ta ya halasta gare shi."[2] Babban malamin Hadisi a wurin 'yan Shi'a, wanda suke ɗaukar sa kamar yadda Ahalus Sunna suka ɗauki Imam Bukhari, watau Muhammad binu Ya'aƙub Alkulaini, shi ma ba'a bar shi a baya ba. Ya ruwaito cewa, Imaminsu na shida Abu Abdillahi Ja'afar Sadiƙ, ya ara wa almajirinsa, Muhammad binu Mudarib, wata kuyanga a lokacin da ya ziyarce shi. Ga abinda almajirin yake cewa: "Abu Abdullahi (A.S) ya ce mini: "Ya kai Muahammad, riƙi wanan baiwa ta yi maka hidima kuma ka shafe ta (ka sadu da ita). Idan za ka tafi, sai ka komo mana da ita."[3]

Duba ka gani ɗan uwa mai karatu, Allah ya tsarshe ni tare da kai daga sharrin 'yan Shi'a da ɓatansu, yadda Rafilawa suka kai matuƙa wajen ƙoƙarin yaɗa lalata da alfasha a tsakanin al'umma ta hanyar halasta zina da ƙira ƙarya a dangana ta ga zaɓaɓɓun bayin Allah.

Mu imaninmu shi ne, wannan ruwaya da aka dangana wa Ja'afar Sadiƙ ƙarya ce aka yi masa. Imam Ja'afar Sadiƙ ba zai bar tafarkin kakansa Annabi(SAW) ba, ya bi tafarkin Majusawa.

## Muhimmiyar Sanarwa

Dukkan littafan malaman Shi'a da muka yi amfani da su wajen rubuta wannan taƙaitaccen littafi ana samun su a laburaren cibiyar **Markazus Sahabah** dake Sakkwato Birnin Shehu, kuma mai son ya ga waɗannan littafai yana iya yin haka ba tere da wata matsala ba. Laburaren buɗe take ga kowa da kowa.

[1] A duba **Al'istibsar** na Aldusi, muj. na 3 sha. na 141.
[2] **Al'istibsar**, muj. na 3 sha. na 136.
[3] A duba **Furu'ul Kafi** na Kulaini, muj. na 2 sha. na 200.